AMPLIFYCHANGE

# Kayan aiki

## Na mai kula da tsarin aikin HKLJH

KUNDI KOYASWA NA 2 : A GANE KUMA A AIKATA YIN TSARI BISA GA HAKI DA YA SHAFI AIKIN HKLJH

**Nazarin Dalilai Dangance da Hakin mutane(NDDH)**




Agusta 2019

# Abin da ke ciki


**Kalmomin farko** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

**1. Gabatarwa** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

- **1.1 Yanayin da ake ciki** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **1.2 Dalili** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **1.3 Manufa** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **1.4 Guri** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **1.5 Matakan tafiyar fa aiki** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **1.6 Abin da kundin ya ƙumsa** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

**2. Ma'anar kalmomi** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

- **2.1 NDDH** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **2.2 Masu hakin** ...... **Erreur ! Signet non défini.**
- **2.3 Masu wajibin tilasa a kiyaye hakin** ...... 8

**3. Fanni uku na fuskantar da cigaba** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

**4. NDDH da bunƙasa HKLJH** ...... 13

**5. NDDH da farilan hakin ɗan Adam** ...... 15

**6. Allon auna tsari da projen HKLJH bisa ga NDDH** ...... 19

- **6.1 Allon auna fanni 4 na kan gaba na NDH cikin tsari/projen HKLJH** ...... 20
- **6.2 Allon auna yanayin tsari/projen HKLJH bisa ga NDH** ...... 22
- **6.3 Allon auna ingancin tsari/projen HKLJH bisa ga NDH** ...... 24
- **6.4 Allon auna ingancin bin sau-da-ƙafa na tsari/projen HKLJH bisa ga NDH** ... 26

**7. Wa ke iya amfani da allon, da kuma yaya za a yi amfani da shi?** ...... 28

**8. Maƙasudi** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

**Abubuwan da ake iya dubawa** ...... **Erreur ! Signet non défini.**

## Kalmomin farko

**Ofishin bada Shawara da tallafi ta fannin Tarbiyya daga Tushe da ake kira (CAEB)** ya san da muhimmancin neman afuwa da ƙarfafa iyawar Ƙungiyoyin Fara Hula game da al'amarin kare Hakin mutane, ta fannin Kiyon Lafiya da ya shafi Jima'i da Haifuwa (HKLJH).

An shimfiɗa dokoki da farilai da yawa na ƙasa da ƙasa domin a tabbatar da hakin ɗan Adam gaba ɗaya, da kuma HKLJH daga cikinsu:

- Jerin ayukan cigaba mai ɗorewa daga nan zuwa 2030 ;
- Kundin Majalisar Ɗumkin Duniya da aka sa hannu a kanshi a Francisco a shekara ta 1945
- Yarjejeniya ta ƙasa da ƙasa da ke kula da Hakin Yara Ƙanana da ake kira (CIDE) ta shekara 1990
- Kundi Hakin ɗan Adam da Al'umma na Afirika da aka shirya a shekara ta 1981
- Yarjejeniya ta Kundi Hakin ɗan Adam da Al'umma mai kula da hakin mata a Afirika, da ake kira « Yarjejeniyar Maputo » na shekara ta 2005.

Bunƙasa NDDH cikin masu aiki cikin fannin HKLJH, mataki ne mai muhimmanci na tabbatar da sa hannun marasa galihu cikin tafiyarda tsarin HKLJH. Yana sa a rabu da tunanin bada taimako shi kaɗai, ko biyan bukatu. Amma yana ba waɗanda aka ware damar su more ma hakinsu kamar kowa.

An shirya wannan kundin koyaswa, domin aiwatar da ayukan proje na Amplifychange da ya shafi ƙasashe 4 na Afirika ta kudancin Sahara (Burkina Faso, Guinée, Mali et Niger). Yana ɗaya daga cikin kundayen koyaswa 4 na «Kayan aikin mai kula da tafiyar da aikin HKLJH» wanda za ya ƙarfafa iyawar shugabannin ƙungiyoyi masu aikin neman afuwa, da suke cikin tsarin bunƙasa HKLJH cikin ƙasashen 4 da aka zaɓa a Afirika ta kudancin Sahara. A cikin kafa ƙungiyoyi masu kula da kare hakin mutane game da kiyon lafiya ta fuskar jima'i da haifuwa, wannan kundin koyaswa za ya ƙarfafa aikin haɗin gwiwa tsakanin ƙungiyar fara hula a cikin ƙasa, da wurare daban-daban. Wannan kundayen koyaswa suna cikin kayan aiki:

- Kundin koyaswa na 1: Yadda ƴan ƙasa ke ɗaukar niyya domin ƙarfafa amfanin da dokoki cikin aikin HKLJH
- Kundi koyaswa na 2: A gane, a kuma yi aiki da tsarin da aka yi bisa hakin mutane cikin fannin HKLJH
- Kundin koyaswa na 3: Shimfiɗa aikin haɗin gwiwa domin neman afuwa na samo ma mutane hakinsu, game da aikin HKLJH.
- Kundin koyaswa na 4: Kayan aikin na gwarzayen aikin waye ma mutane kai a kan aikin HKLJH, a cikin makarantu ko wasu wurare daban.

Abin da kundayen koyaswar suka ƙumsa, yana lura da yanayin siyasa, da zamantakewa, da tattalin arziki na ƙasashen, da yankunan ƙasashen, da kuma matsaloli da suka zama kangi ga aikin HKLJH, bisa ga bincike daban-daban da muka yi[1] da kuma abin da abukan aikinmu na cikin sauran ƙasashe suka ji kuma suka gani.

Kowane kundin koyaswa na kayan aiki, an shirya shi yadda za ya zama da sauƙin amfani da shi, inda akwai jagoran koyaswa na kundi cikin siffar PDF da Word, da PowerPoint na kundin, domin bukatun koyaswa nan gaba cikin ƘFH, da bidiyo da aka ɗauka tamkar misali mai kyau na masu koyar da ƘFH.

An shirya kayan aikin cikin harshe faransanci, aka kuma juya su cikin harsuna 4 (Bambaranci na Mali, Maninka na Guinée, Hausa na Niger et Mosanci na Burkina Faso) da kuma rubuntu makafi da ake kira Braille.

Muna fatan wannan kundayen koyaswa za su taimaka ma masu tafiyar da tsarin aiki na ƙungiyoyin da ke aikin bunƙasa HKLJH, su ƙware a cikin aikin kuzarantar da mutane, da sarrafa kuɗi da aka zuba domin kawasda ƙalubalan da suka shafi aikin HKLJH , tare da tabbatar da sa hannun marasa galihu cikin aikin.

[1] Les 11 études menées par Ebenezer International dans le cadre de la présente subvention stratégique sont les suivantes:

- Six (6) Analyse de l'Economie Politique du secteur DSSR respectivement au Burkina Faso, Mali, Niger, Guinée, Malawi, Zimbabwe, disponible en français. La version Anglaise est aussi disponible pour les études du Malawi et du Zimbabwe ;
- Analyse comparative ciblée de la littérature en lien avec les DSSR en Afrique de l'Ouest (Burkina Faso, Mali, Niger, Guinée), disponible en française ;
- Analyse comparative ciblée de la littérature en lien avec les DSSR en Afrique du Sud-Est (Malawi, Zimbabwe, Ouganda, Afrique du Sud), disponible en français et en anglais ;
- Sondage en ligne sur la satisfaction des citoyens sur les Droits à la santé sexuelle et reproductive pour les écoles secondaires et les universités avec 30 000 répondants dans 6 pays de l'Afrique subsaharienne (Mali, Burkina, Niger Guinée, Malawi, Zimbabwe) disponible en français ;
- Analyse de l'indice du pays favorable aux DSSR pour 6 pays de l'Afrique subsaharienne (Mali, Burkina, Niger Guinée, Malawi, Zimbabwe), disponible en français;
- Rapport sur la performance des droits à la Santé Sexuelle et Reproductive pour 6 pays de l'Afrique subsaharienne, disponible en français ;
- Formulaire d'évaluation de la performance des politiques DSSR, disponible en français.

# 1. Gabatarwa

## 1.1 Yanayin da ake ciki

Ƙasashen Afirika ta Yamma da Yankin Kudanci Afirika, suna fuskatanr ƙalubalai da yawa: matsalolin yin aiki da dokoki, matsalolin fassara su, haɓakar ci da haikin mutane, matsalolin da suka zama kangi game da harakar magani, kasawar tabbatar da hakin mutane, rashin isassun kuɗi domin tafiyar da aikin kiyon lafiya, rashin daidaitattun farilai na aikin (HKLJH), bisa ga yadda ƙasashen duniya suka ɗauki alkawari.

AmplifyChange tana da gudummawa mai dubaru da ke da gurin :

- A nemi afuwa, kuma a taimaka wajen inganta siyasa da dubarar aikin HKLJH, dangance da abubuwa (darusa) na kan gaba na AmplifyChange cikin yankunan ƙasashe, cikin ƙasashe 4 na Afirika ta Yamma (Mali, Guinée, Niger, Burkina Faso) ;
- A sauƙaƙa ƙarfafa iyawar mutane game da kafa aikin haɗin gwiwa na ƙungiyoyin fara hula, domin iya aiwatar da aiki mafi kyau, bi sau-da-ƙafa na tasirin da siyasar aikin HKLJH cikin ƙasashen 4 na Afirika ta kudancin Sahara a Afirika ta Yamma (Mali, Guinée, Niger, Burkina Faso).

Banda wannan, projen yana aiki tare da ma'aikatu biyu cikin Afirika ta Yamma da Yankin Kudancin Afirika, wato:

- Ƙungiyar Kiyon Lafiya ta Afirika ta Yamma da ake kira (OOAS) a cikin Haɗin Kan Ƙasashen Afirika ta Yamma ta fannin Tattalin Arziki da ake kira (CEDEAO) a Bobo Dioulasso, a ƙasar Burkina Faso;
- Asusun Majalisar Ɗumkin Duniya mai Kula da Al'umma (UNFPA), mai cibiyarsa a Afirika ta Yamma a Dakar, ƙasar Sénégal.

Wannan gudummawa mai dubara ta AmplifyChange aikin haɗin gwiwa na ƙungiyoyi 4 (CAEB, Haɗin gwiwar ƘFH domin sake salon tafiyar da tsarin iyali a Afirika ta Yamma mai aikin da harshen faransanci, Ebenezer International et Humanité & Inclusion) domin tsawon shekara biyu ( 2 ) , daga 1 ga watan Nobamba na 2018 zuwa 31 ga watan Oktoba na 2020, inda **CAEB** ce ke shugabanci. Tana ba ƙungiyoyin da ke cikin wannan ƙawance damar su yi aikin neman afuwa, su kuma tafiyar da ayukan ƙarfafa iyawar ƙungiyoyi domin a inganta siyasar aiki da dubarun HKLJH, cikin ƙasashe 4 na Afrika ta kundanci Sahara a Afirika ta Yamma (Mali, Niger, Guinée da Burkina Faso), tare da kan ziyara ta musanyar bayanai da kwatanta binciken da aka yi cikin ƙasashen Yankin Kudancin Afirika (Malawi, Zimbabwe da Ouganda).

An aiwatar da projen cikin yankunan ƙasashe biyu na Afirika ta kundancin Sahara :

- Afirika ta Yamma: Guinée, Mali, Niger, Burkina Faso ;
- Yankin Kudancin Afirika : Malawi, Zimbabuwe, Ouganda.

### 1.2 Dalili

Ta wannan dalili ne aka shirya waɗannan kundayen koyaswa huɗu na «Kayan aiki na mai kula da tafiyar da tsarinHKLJH ». An zaɓi kundi koyaswa na 2, mai suna « Ganewa da shirya tsari dangance hakin mutane cikin fannin HKLJH », domin a yaɗa al'amarin fuskantar cigaba dangance da hakin mutane, masamman tsakanin masu aikin bunƙasa HKLJH.

### 1.3 Manufa

Wannan kundin koyaswa yana nufin a gabatar da NDDH ga masu tafiyar da tsarin HKLJH na abukan aikinmu masu aiki cikin fannin HKLJH. Yana ba su kayan aiki na auna tsari da projensu a kowane mataki (shiryawa, aiktawa, bin sau-da-ƙafa), domin a tabbatar da suna aiki da farilai da ka'idodin NDDH. Manufar ƙarshe ta kundin, ita ce tabbatar ma marasa galihu da waɗanda aka ware, su more da HKLJH yadda ya kamata, a Mali, da Guinée, da Burkina Faso da Niger.

### 1.4 Guri

Wannan kundi yana sa masu kula da tafiyar da tsari da projen HKLJH su yi abubuwa kamar haka :

- Su saba da NDDH, da duk wasu abubuwa da suke da nasaba da haka;
- Su iya bambanta hanyoyin nan uku na fuskatar cigaba, su kuma ga muhimmancin NDDH domin cikakkiyar bunƙasawar HKLJH mai ɗorewa;
- Su sansance da nasabar da ke akwai tsakanin NDDH, da hakin ɗan Adam dangance da fannin HKLJH;
- Su iya aiki da allo na auna fannonin nan huɗu na kan gaba mafiya muhimmanci na NDDH, cikin tafiyar da tsari da projen HKLJH.

### 1.5 Hanyar tafiyar da aiki

A shirya wannan kundin koyaswa bisa ga tafarkin sa hannun kowa da kowa, daidai da wannan hanyar tafiyar da aiki, mai matakai huɗu :

- **Mataki na 1 :** zaɓen mashahurin da za ya ƙirƙiro kundin farko;
- **Mataki na 2 :** Neman littattafai da munsanyar bayanai tsakanin jigajigan masu akin cikin HKLJH;
- **Mataki na 3 :** Yin amfani da shawarwari da aka samu cikin binciken da aka tafiyar da shi ƙarƙashin Ebenezer International;
- **Mataki na 4 :** Yin amfani da ƙarin bayanai da aka samu cikin wallafawar ƙarshe ta kundin.

### 1.6 Abin da kundin ya ƙumsa

An tsara abin da kundin ya ƙumsa da sashe uku na koyaswa, kamar yadda aka gabatar da su a nan:

- **Sashe na 1 : Ma'anar kalmomi**

An fara da bada ma'anar ko minen NDDH, da ta ko su wanene suke da hakin, ko masu wajibin tilasa a kiyaye hakin. Yana bada ma'anar su wanene marasa galihu, mutanen da aka ware, kafin a fara zancen hakin mutane da farilansa.

- **Sashe na 2 : Hanyoyi uku na fuskantar cigaba**

Wannan sashe na gabatar hanyoyin uku, wato: hanya ta nuna jinƙai, ta biyan bukatu, da ta kiyaye hakin mutane; dukansu cikin allo mai kwatanta su.

- **Sashe na 3 : NDDH da HKLJH**

Wannan sashe na gabatar da HKLJH tamkar hakin mutane da ake kiyayewa ko'ina, wanda ba su rabuwa, ba a iya musun su, kafin a zana wasu daga cikinsu. Bayan wannan ya gabatar da amfanin NDDH cikin HKLJH.

- **Sashe na 4 : NDDH da Hakin ɗan Adam**

Wannan sashe yana gabatar da NDDH da nasabar da yake da da farilan hakin ɗan Adam, da aiki da su. Yana sa hakin ɗan Adam cikin fannonin da ake aiki. Yana ƙarewa da Farilan hakin ɗan Adam da yadda ake aiki da su cikin HKLJH.

- **Sashe 5 : Allon auna fannoni 4 na kan gaba na NDDH**

Wannan sashe yana gabatar alluna (4) da suke sa a auna abubuwa kamar haka :

- Fannoni 4 na kan gaba mafiya muhimmanci na NDDH a cikin tsari/projen HKLJH;
- Fannoni 4 na kan gaba na NDDH a cikin yanayin tsari/projen HKLJH;
- Ingancin tsari/projen HKLJH dangance da fannoni 4 na kan gaba na NDDH ;
- Ingancin aikin bin sau-da-ƙafa na tsari/projen HKLJH dangance da fannoni 4 na kan gaba mafiya muhimmanci na NDDH.

## 2. Ma'anar kalmomi

### 2.1 NDDH (Nazarin Dalilai Dangance da Hakin mutane)

Fuskantar al'amarin cigaba wadda ta kafu bisa lura da hakin ɗan Adam, yanayi ne wanda ke amfani ka'idodi da farilai, da guri irin na ƙasa da kasa da suka shafi hakin ɗan Adam cikin tafiyar da aikin cigaba. Wannan hanya tana da matakai da ayuka da suke haɗa sha'anin hakin ɗan Adam da sha'anin iko da kokowa da cigaba.

Zance masu wajibin tilasawa da masu hakin, suna da muhimmanci dangance da hakin ɗan Adam. Sani da zaman masu amfana da tsari/projen HKLJH a matsayinsu na waɗanda ke da hakin, yana tilasa ma masu tafiyar da tsarin HKLJH su daidaita aikinsu da farilan da duniya ta tsaida dangance da kiyayewa, da kariya na hakin ɗan Adam.

A cikin fannin HKLJH, lura da kiyaye hakin ɗan Adam abu ne mai amfani, idan aka yi aikata bisa gare shi. Yana sa a sansance da ƙalubalai da matsalolin na masamman da marasa galihu ke fuskanta cikin neman samun bayanai da kulawa ta fannin kiyon lafiya da ya shafi jima'i.

Hanyar fuskantar cigaba da ta kafu bisa ga kiyaye hakin ɗan Adam, tana bukatar tunani mai zurfi game da kiyayewa da kariyar hakin waɗannan gungun marasa galihu. Haka kazalika ana bukatar a yi aiki tare domin a magance manyan dalilai da suke sa bambanci, da hana kai ga samun biyan bukata, da wariya, da taka hakin ɗan Adam da ake yi cikin sha'anin kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa.

Ya kamata a yi amfani da hanyar fuskantar cigaba, da ta kafu bisa ga kiyaye hakin ɗan Adam, a kowane mataki na tafiyar da tsari/proje na kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa zuwa ga marasa galihu.

### 2.2 Waɗanda suke da haki

| |
|---|
| Kowane ɗan Adam yana da haki. Wanda yake da haki :<br>• Yana da hakin a ba shi hakinsa ;<br>• Yana da hakin ya yi amfani da hakinsa;<br>• Yana da hakin ya tambayi masu wajibin tilasawa ;<br>• Yana da wajibin ya kiyaye hakin waɗansu. |

### 2.3 Masu wajibin tilasawa

Akwai masu wajibin tilasawa iri biyu: masu tilasawa bisa ga doka, da masu tilasawa bisa ga sanin ya kamata.

#### 2.3.1 Masu tilasawa bisa ga doka

Masu tilasawa bisa ga doka, su ne *waɗanda ya zama tilas gare su, su sa a kiyaye, a kare, kuma a tabbatar da haki ga mai shi.*

*Ta haka, wajibin kiyaye abin da ke tilas dangance da hakin ɗan Adam, ya rataya ga gwamnati. Wannan wajibi ya shafi dukan sassa na gwamnati, kamar su majalisu,*

*ofishin ministoti, malaman makaranta, ko masu aikin yaɗa bayanai, jami'an shari'a, hukumomin doka, ƴan sanda. Dukansu suna da wajibi bisa ga doka.*

Gwamnatoti suna da wajbin su tabbatar da an ba kowa sa'a, ta wurin lura da cewa dukan mutane suna da sa'a iri guda dangance da aikin cigaba. Samun sa'a iri guda na sa marasa galihu su kawas da rashin sa'a, su zama daidai da kowa a cikin al'umma, dangance da more ma aikin HKLJH. Wannan samun sa'a iri guda, ba ya yiyuwa, sai in gwamnati ya sa hannunsa sosai ta fannin daban daban.

#### 2.3.2 Masu wajibin tilaswa bisa ga sanin ya kamata

Kowane mutum da yake da haki, da yake da wajibin kiyaye hakin sauran mutane; ana iya cewa duk mutum ko ma'aikata da take da ikon faɗa a ji game da rayuwar wanɗanda ke da haki, to ya/ta zama mai tilasawa bisa ga sanin ya kamata.
Ta haka, masana'antu masu zaman kansu, shugabannin wuri, ƙungiyoyin fara hula, ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa, masu gidaje da iyaye, da duk dai kowane mutum, sun zama masu tilasawa bisa ga sanin ya kamata.

Gwamnati, a matsayinsa na mai tilaswa bisa ga doka, yana da wajibin bida masu tilasawa bisa ga sanin ya kamata. Misali: iyaye, masana'antu, ds. – ya lura da cewa suna kiyaye hakin ɗan Adam.

### 2.4 Marasa galihu [2]

Kalmar marasa galihu tana nufin mutane waɗanda (shekarunsu, jinsinsu, halin zamantakewarsu da na tattalin arzikinsu, ƙabilarsu, jikinsu, da hankalinsu, ds.) na iya zama wani babban hatsari cikin yanayin tsaro marar inganci (yaƙe-yaƙe, rikici cikin al'umma, allobar yunwa, lokutan tashin hankali, ds.).

Marasa galihu na iya zama mutane ko al'umma masu fusktantar hatsari, marasa sa'a, da suke bukatar ƙara yin ƙoƙari domin su wanzu cikin al'umma su sami cigaba. .

Misalin marasa galihu, ana iya zana: tsofofi, nakasassu, mataye, ƴan gari, gungun kaɗannan mutane, da baƙin haure.

Ta dalilai da yawa, irin waɗannan mutane na bukatar su kawas da wasu matsaloli domin su sami riba zaman rayuwa ko su cimma wani guri dangance da HKLJH, alhali ba haka yake ba ga sauran ƴan ƙasa.

---

[2] http://www.operationspaix.net/67-lexique-groupes-vulnerables.html

## 2.5 Mutanen da aka ware ko aka manta da su

### 2.5.1 Mutumen da aka ware[3]

**Mutumen da aka ware,** « mutum ne da aka yasda shi, aka kore shi daga cikin wani gungu, ko ƙungiya, ma'aikata da yake ciki. » Wannan kalma ce da aka yi amfani da ita a ƙarshe shekara 1980, wadda take nufin dukan mutanen da suke ƙasa ga ma'aunin talauci.

### 2.5.2 Mutumen da aka ware/manta da shi

Amma, mutumen da aka manta da shi, shi ne «wanda aka maida dabra ga al'umma, wanda babu shi cikin duk abin da ke wakana cikin al'umma ». Sassan al'umma ne ke maida wasu mutane dabra.

## 2.6 Hakin ɗan Adam

> [4]Hakin ɗan Adam, haki ne da ba za a hana ma kowane ɗan Adam ba, ko shi na wace ƙasa ne, wurin zamansa, jinsinsa, asulin ƙabilarsa ko ƙasarsa, launin fatarsa, addininsa, ko duk wani hali daban.

Hakin ɗan Adam na ko'ina, ana sa shi cikin doka, a rubuce cikin wani kundi, ko haki bisa ga al'adu na ƙasa da ƙasa, ko wasu farilai da wasu masamar haki irin na ƙasa da ƙasa. Doka ta ƙasa da ƙasa dangance da hakin ɗan Adam tana cewa wajibi ne ga gwamnatoti su yi wasu abubuwa, ko su ƙi, domin a kare haki da ƴancin waɗansu mutane.

### 2.6.1 Na kowa a ko'ina, wanda ba a iya musantawa.

**Na kowa a ko'ina :** Gwamnatoti suna da wajibin su inganta kuma su kare hakin ɗan Adam da ƴancinsa, a cikin kowace irin aƙida siyasa, tattalin arziki, ko al'adu.

**Wanda ba ya musantuwa :** Ba a iya sake shi, sai ko cikin wani yanayi na masamman dangance da wasu ƙayyadaddun matakai. Misali ana iya taƙaita ƴancin haki mutum, idan shari'a ta tuhume she da mugun laifi.

### 2.6.2 Sarƙe cikin juna har da ba a iya raba su.

Dukan hakin ɗan Adam daban daban ba a iya raba su, ko ta fuskar zama ɗan ƙasa ko ta fuskar siyasa, masamma hakin rayuwa, zama daidai gaban doka, da ƴanci mutum na ya faɗi abin da yake so; haki ta fannin tattalin arziki, zamantakewa da al'ada, aiki, tsaro da zaman lafiya, tarbiyya; ko wani haki na taro kamar hakin cigaba da hakin bayyana kai. Dukan wannan haki daban daban suna harhaɗe, har da ba a iya raba su. Inganta wani haki, yana sa wasu su sami hakinsu. Haka kazalika, hana wani haki yakan ɓata wasu.

---

3 https://www.larousse.fr/dictionnaires/francais/exclu_exclue/32016

4 https://www.ohchr.org/FR/Issues/Pages/WhatareHumanRights.aspx

### 2.6.3 Daidai, kuma babu wariya

Farilar rashin nuna wariya game da hakin ɗan Adam da ƴancinsa, ta shafi kowa da kowa, kuma ta hana duk wata wariya bisa ga abubuwa kamar: jinsi, asuli, launin fata, ds. Wannan farila tana biye da farilar daidaici tsakanin mutane, da yake cikin ayar doka ta farko ta Furcin ƙasa da ƙasa na hakin ɗan Adam: "Dukan ƴan Adam, akan haife su ƴantattu cikin mutunci da hakinsu".

### 2.6.4 Haki da wajibi[5]

**Haki daban daban :** Haki na ƙasa da ƙasa yana tilasa ma gwamnatoti su sa a kiyaye, a kare kuma a tabbatar da hakin ɗan Adam. **Kiyaye hakin ɗan Adam** na nufin kada gwamnatoti su hana a ba ɗan Adam hakinsa. **Karewa** nufin cewa ya kamata gwamnatoti su kare mutane, da gungun mutane domin kada a taka hakinsu. **A tabbatar da** na nufin ya kamata gwamnatoti su ɗauki matakan da suka dace domin sauƙaƙa ba ɗan Adam hakinsa.

**Wajibi :** A matsayin kowane mutum, lalle muna da haki mu more ma hakinum, amma kuma muna da wajibin kiyaye hakin wasu.

[5] https://www.ohchr.org/FR/Issues/Pages/WhatareHumanRights.aspx

### 3. Hanyoyi uku na fuskantar cigaba

Domin a iya aiki da NDDH cikin tafiyar da tsarin HKLJH, yana da kyau ga masu kula da tafiyar da tsarin proje su gane ko minene bambanci tsakanin wannan hanya, da sauran hanyoyin biyu na fuskantar cigaba, inda suka kafu bisa nuna jinƙai, biyan bukatu, ba bisa ga hakin mutane ba. Wannan allo yana gabatar da fassara mai kwatanta hanyoyin uku.

| Bisa ga nuna jinƙai | Bisa ga biyan bukatu | Bisa ga kiyaye hakin mutane |
|---|---|---|
| Ana maida hankali ga abin da ake samu, ba ga sakamako ba | Anda maida hankali ga abin da ake samu da kuma sakamako | Ana maida hankali ga matakai da sakamako |
| An fi maida hankali ga nuna jinƙai | Ana maida hankali ga samun biyan bukatu | Ana maida hankali ga more ma haki da mutane suke yi |
| An san da wajibin sanin ya kamata na masu arziki zuwa ga talakawa | Ana ganin bukatu tamkar roƙo na ainahi | An san da hakin mutane da gungun mutane tamkar kira ga a ba su hakinsu wurin waɗanda ke tilasawa a yi haka ɗin |
| Ana ganin mutane tamkar waɗanda aka yi masu wani lahani | Mutane su ne dalilin aikin cigaban da ake yi | Mutane suna samun ƙafafawa domin su ƙwato hakinsu |
| Mutane sun cancanci a agje su | Mutane sun cancanci a agaje su | Mutane suna da hakin a agaje su |
| Ana maida hankali ga bayyanuwa matsaloli | Ana maida hankali ga dalilan farko na matsaloli | Ana maida hankali ga dalilai na ainahi da bayyanuwarsu |

## 4. NDDH da bunƙasa HKLJH

### 4.1 NDDH da HKLJH

Hakin Kiyon Lafiya da ya shafi Jima'i da Haifuwa (HKLJH), haki ne na ɗan Adam da ake aiki da su ko'ina; ba sa rabuwa kuma ba a musunsu. HKLJH ya kafu bisa a wasu hakin ɗan Adam – kamar haki ta fannin kiyon lafiya, rayuwa, hakin ba za a yi ma mutum zilama da wariya ba. Wannan duka haki ne wanda ake tabbatar da shi cikin yarjejeniya ƙasa da ƙasa, cikin dokoki da siyasar ƙasashe. Ƙungiyoyi masu kula da hakin ɗan Adam da suke da iko, kamar irin su tsarin lura da kiyaye yarjejeniya ta Majalisar Ɗumkin Duniya, Mashari'antu na ƙasashe daban daban, da kotun ƙoli na dokokin ƙasa – sun fassara kuma sun sa hakin ɗan Adam cikin al'amarin kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa.

Daga cikin hakin da ya shafi al'amarin jima'i da haifuwa na marasa galihu, ko waɗanda aka ware ko aka manta da su, da suke bukatar lura ta masamman cikin tafiyar da tsarin HKLJH, ana iya zana waɗannan:

- Hakin zama daidai da kowa ;
- Hakin sa hannu cikin duk wani aiki;
- Hakin rayuwa, da na hana a taka hakin mutum ;
- Hakin na rayuwar sirri;
- Haki na ƴancin kai da na samun sanuwa daga doka;
- Hakin tunani da faɗin abin da mutum ke so;
- Hakin zama da lafiya;
- Hakin mutum ya sani, kuma ya koya;
- Hakin mutum ya zaɓa ya yi aure ko ya ƙi, ko ya sami ƴaƴa ko ya ƙi;
- Hakin ya sa a kiyaye hakinsa.

### 4.2 Ribar da NDDH take kawowa cikin fannin HKLJH

A cikin aikin NDDH, talauci ba rashin kayan aiki kaɗai ba ne, ko kuma rashin warware matsaloli yadda ya kamata. A ƙashin gaskiya, ko da akwai kayan aikin, ana hana ma marasa galihu su kai gare su ta dalilin asulinsu, wurin zamansu, ko kuma wani lokaci ta dalilin rashin kulawa ko rashin ganin akwai wata riba. Irin wannan wariya na iya zama abubuwan da ke sa a yi ƙyamar su, kuma a manta da su tun daga farko, a cikin al'umma, cikin gidaje, ko kuma cikin al'amarin siyasa. Yana iya zama tushen rashin daidaici cikin sha'ani doka, ko ta fuskar hakin ɗan Adam. A cikin irin wannan hali, talauci ya zama abin da aka tilasa ma mutane kenan. Ana iya cewa kenan, mutane ba talakawa ba ne , amma suna talautadda kansu. NDDH ya kafu bisa ga tunanin cewa ya kamata a kare mutanen da aka talautar da su, daga wariya ta rashin gaskiya, da ƙwace, da hana masu ƴancin ɗaukar ƙuduri, ds.

Ribar da NDDH ke kawowa zuwa ga fannin HKLJH, ana iya cewa yana :

- Bada dama a warware matsalolin kiyon lafiya ta fannin jima'i da haifuwa da suka shafi talakawa da marasa galihu;
- Gane talauci, bai wai halin da mutum yake ciki ba shi kaɗai, amma har cikin yanayin al'umma, gwamnati da al'ummai na ƙasa da ƙasa ;

- Bada damar a maida hankali ga dalilan talauci na ainahi, ta wurin maida hankali ga wajibin masu tilasawa cikin biyan bukatun HKLJH;
- Bada damar kyakkyawan tsinkaye game sha'anin talauci, ta wurin maida hankali ga yadda za a daidaita ƙarfin mutane da siyasa, ta wurin kula da dukan irin hakin ɗan Adam da suka zama marasa rabuwa da musantuwa;
- Bada dama a san cewa ya kamata, ta wurin yanayin cigaba na tare da aka san da shi ko'ina cikin duniya;
- Yarda da taimaka ma gwamnatoti su cika wajibinsu na ƙasa da ƙasa zuwa ga ƴan ƙasa banda wariya;
- Ƙarfafa ƴancin kai ta wurin kafa hulɗa tagari tsakanin sassan gwamnati da gungun mutane, da mutum karan kansa;
- Da iyawa mai yawa domin kawo sakewa tagari cikin rayuwar mutane, ta wurin aikin da ya yi, na kula da rashin adalci, da bambanci, da wariya, da ɗauka alhaki, da hana ma mtuane hakinsu.

## 5. NDDH da farilan hakin ɗan Adam

### 5.1 NDDH da farilan hakin ɗan Adam

NDDH, hanya ce da ta ƙumshi farilai da ƙa'idodin haikin ɗan Adam na ƙasa da ƙasa, cikin aikin cigaba. Majalisa Ɗumkin Duniya ce ta kawo wannan ganewa ta NDDH, inda aka jera wasu manyan farilai na hakin ɗan Adam da suke da nasaba da aikin cigaba.

Yawancin jerin farilan suna iya sakewa kaɗan, amma yawanci lokaci suna tsare domin tabbatar da adalci ga kowane mutum. Ga yadda farilan suke:

- Hakin ɗan Adam ba ya musantuwa, ba su rabuwa,
- Ƴanci da sa hannu cikin aiki
- Daidaici da rashin wariya
- Wajibi

### 5.2 Fannoni huɗu na aikin NDDH

Aikin da farilan hakin ɗan Adam cikin tafiyar da aikin cigaba, ya zama babban tushe na RBA. Ko da shike farilan suna da ƙarfi, ƙungiyoyi da yawa suna ganin cewa suna da wuyar aikatawa. A matsayinsu na farilai, sun zama ginshiƙi da jagora. Suna bayyana sanin ya kamata, kuma ya kamata a aikata bisa gare su.

Ma'aikata ta Danemark ta shirya wannan farilai cikin fannoni huɗu na aiki, da suke bida ƙoƙarin tafiyar da tsarin NDD, da irin yadda ake aikata su cikin aikin cigaba. Wannan fannoni su ne:

- Gungun mutane mafiya rashin galihu ;
- Dalilai na ainahi;
- Masu haki da masu wajibin tilasa kiyaye hakin ;
- Iya yi wa kai.

Maida hankali bisa ga marasa galihu, har da matsalolin da suke da nasaba da jinsi da wariya, ana ganin su cikin:

- Ƙoƙarin aikin cigaba da yake nufar marasa galihu, da waɗanda aka ware su;
- Aikin cigaba da yake maida hankali ga sha'anin rashin galihu da wariya da ake nuna ma mutane ta fannin siyasa (ko rashin siyasar), da mahukunta na wuri, da tabi'o'in al'adu.
- Dubarun cigaba inda ake bayyana abin da aka cimma, da abin da ba a yi ba, da kuma waɗanda aka manta da su.

Maida hankali ga dalilan talauci na ainahi, da taka hakin ɗan Adam na bayyanuwa cikin :

- Tsarin cigaba inda ake fassara bukatun da ake ciki, da kuma wajibin al'mma na kiyaye hakin ɗan Adam.
- Fuskantar sha'anin cigaba gaba ɗaya tare da lura da hakin ɗan Adam.
- Cigaban da ba ya duba inganta tattalin arziki kaɗai, amma wanda yake kula da mutane da iyawarsu ta tabbatar fa hakinsu da ƴancinsu.

- Ƙoƙarin cigaba da yake tunkarar matsaloli, yayin da ake warware su a matakin wuri, cikin ƙasa da cikin ƙasashe.

Maida hankali ga hulɗa tsakanin masu hakin da masu wajibin su tilasa a tabbatar da hakin, ya ƙumshi:

- Tsarin cigaba wanda yake lura da shawarwarin ƙungiyoyin kare hakin ɗan Adam na ƙasa da ƙasa;
- Ya kamata aikin cigaba ya san da cewa masu amfana da aiki su ne masu haki, ya kuma ba su iyawar ƙwato hakinsu.
- Ya kamata aikin cigaba ya nufi iyawar masu wajibin tilasa a kiyaye hakin ɗan Adam, domin su cika wajibinsu zuwa ga masu hakin.
- Ya kamata masu aikin cigaba su yi amfani da dokoki da siyasar aiki domin su sa masu tilasawa su cika wajibinsu.
- Ƙoƙarin aikin cigaba wanda da zai shimfiɗa matakai na doka, da za su ƙarfafa bada lissafi, irin wanda zai ba ƴan ƙasa damar su sami hakinsu.

Iya yi wa kai na nufin :

- Ya kamata aikin cigaba ya haɗa da masu amfana, da abukan aiki, a lokacin ɗaukar ƙuduri game da dubaru da guri game da cigaban.
- Ba ya kamata aikin cigaba ya ɗauki sa hannun mutane cikin aiki tamkar kayan aiki ba, amma tamkar gurin aikin cigaba.
- Bada lissafi ba sha'anin sakamakon cigaba kaɗai ba ne, amma ya shafi matakan da ake bi da kuma ƙungiyoyin da suke tafiyar da aikin.
- Ya kamata cigaba ya bunƙasa ƙawancen ƙungiyoyi da ƙarfafa mutane su sa hannusu cikin shugabanci, domin su iya ƙwato wa kansu hakinsu.

Maida hankali ga waɗannan fannoni huɗu – marasa galihu, dalilai na ainahi, masu haki da masu wajibin kiyaye shi, da iya yi wa kai – yana da tasiri bisa ga dukan matakan tsarin NDDH.

### 5.3 Farilan hakin ɗan Adam da yadda ake aiki da su cikin HKLJH.

Wannan allo yana gabatar da farilai da aka fi aiki da su game da sha'anin hakin ɗan Adam, da yadda ake amfani da su cikin HKLJH, kamar yadda Ofishi mai lura da hakin ɗan Adam na Ƙunigiyar Kiyon Lafiya ta Duniya ya tsara..

| Farilan hakin ɗan Adam | Yadda ake aiki da su cikin HKLJH |
|---|---|
| Babu nuna wariya | • Bada kulawa ta fannin hanyoyin hana ɗaukar juna biyu ga kowa da kowa, banda nuna wariya, tilasawa ko zilama<br>• A lura da mutanen da aka ware/manta da su, waɗanda ba su samun kai ga samun kulawa ta fannin hanyoyin hana ɗaukar juna biyu |

| Farilan hakin ɗan Adam | Yadda ake aiki da su cikin HKLJH |
|---|---|
| Akwai kayan aiki | • A tabbatar da akwai zaɓi da yawa na hanyoyin hana ɗaukar juna biyu domin kowa da kowa, har da na gaugawa |
| Ana iya kai ga wuraren samun kulawa | • A bada cikakkiyar tarbiya ta fannin jima'i, wadda ta yi daidai da abin da kimiyya take koyas, masamman zuwa ga marasa galihu.<br>• A kawasda matsalolin kuɗi da suka zama kangi ga aiki kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa, domin marasa galihu<br>• A inganta samun kulawa ta fannin kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa domin waɗanda suke da matsalar kai ga samun kulawar<br>• A tabbatar da kulawa tana kai ga waɗanda suka bar muhallinsu, da kuma waɗanda ci ma zarafi ta fannin jima'i.<br>• A sa aikin kulawa ta fannin hana ɗaukar juna biyu cikin sauran ayuka na kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa, har da al'amarin Ƙanjimau, lafiyar uwa da jariri, da kulawa bayan an sami zubda ciki.<br>• A yi amfani da mai'akatu masu yawo domin kulawa da marasa galihu ta wurin ba su bayanai<br>• A yi aikin neman afuswa domin kyautata kawas da abubuwan da ke hana matasa marasa galihu su sami kulawa, waɗanda suke da nasaba da dokoki da siyasa. |
| Abin da aka yarda da shi | • A ba marasa galihu shawarwari game da sha'anin hana ɗaukar juna biyu<br>• A lura da cikas ɗin ke biyo bayan a sha magani, cikin kulawar da ake yi<br>• A kai marasa galihu wani wuri, idan ba a samun kulawa a inda suke |
| Inganci | • A shimfiɗa matakai na tabbatar da ingantacen aikin HKLJH domin marasa galihu.<br>• A kafa aikin kulawa domin a riƙe ko a fidda mutane daga cikin tsarin, da bada shawarwari dangance da hana ɗaukar juna biyu wanda ke iya warwarewa cikin tsawon lokaci a wuri guda.<br>• A ci gaba da koyas da marasa galihu bisa ga aikin kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa<br>• Akwai ma'aikata da suka ƙware cikin aikin da suke saduwa da marasa galihu da suke bukatar kulawa |
| Ɗaukar ƙuduri cikin sanin abin da ake ciki | • A bada cikakkun bayanai a kan hana ɗaukar juna biyu, tarbiyya da shawara domin a tabbatar da marasa galihu suna iya zaɓi mai kyau<br>• A tabbatar da marasa galihu suna iya zaɓi mai kyau gaban kansu, game da amfani da hanyoyin hana ɗaukar juna biyu na gaugawa, masu aiki ɗan lokaci kaɗan, mai dogon zango, ko na dindindin, banda nuna wariya. |

| Farilan hakin ɗan Adam | Yadda ake aiki da su cikin HKLJH |
|---|---|
| Riƙe sirri | • A kiyaye da cewa an kare rayuwar marasa galihu, da takardunsu na likita, da bayanai a kansu |
| Sa hannu cikin aiki | • A ba marasa galihun tsarin ya shafi damar su sa hannunsu cikin aikin yadda ya kamata, cikin shirya proje, da aiwatar da shi, da bi sau-da-ƙafa, da bada lissafi |
| Bada lissafi | • A shimfiɗa matakan bada lissafi na ƙwarai cikin aikin kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa, da bada bayanai, da bi sau-da-ƙafa, har da kan ƙara/gyara, ko daga mutum, ko daga irin yadda ake tafiyar da aikin. |

## 6. Allon auna tsari da projen HKLJH bisa ga NDH

Wannan sashe na gabatar da allo iri uku kamar haka:

- Allon auna fannoni huɗu na kan gaba mafiya muhimmanci na NDDH cikin tsari da projen HKLJH;
- Allon auna fannoni huɗu na kan gaba mafiya muhimmanci na NDDH cikin yanayin tsari/projen HKLJH;
- Allon auna ingancin tsari/projen HKLJH dangance da fannoni huɗu na NDDH;
- Allon auna ingancin matakan bin sau-da-ƙafa na tsari/projen HKLJH dangance da fannoni huɗu na kan gaba mafi muhimmanci na NDDH.

Kowane allo yana ƙumshe da fannoni huɗu na kan gaba mafi muhimmanci na NDDH: maida hankali ga gungun marasa galihu, maida hankali ga dalilai na ainahi, aiki da masu hakin, da kuma masu wajibin tilasa shi, da maida hankali ga iya yi wa kai. Cikin kowane fannin an auna alamu biyar (5) ta wurin bada lamba 0 zuwa 5, kanan ƙarin bayani ya biyo baya.

Dangance da masu tafiyar da tsari da projen HKLJH, alluna huɗu na auna wannan sashe suna bada damar amasa tambayoyi kamar haka:

1) Aiki da fannoni 4 na kan gaba mafiya muhimmanci na NDH: Ko shirin tsari/proje yana sa fannonin huɗu na kan gaba mafiya muhimmanci na NDH?
2) Nazarin yanayin da ake ciki: Ko nazarrin yanayin tsari/projen yana sa fannoni 4 na kan gaba mafiya muhimmanci na NDH?
3) Ingancin tsari/proje: Ko abubuwan da tsarin ya ƙumsa suna aiki sosai da fannonin nan 4 na kan gaba mafiya muhimmanci na NDH?
4) Aiwatarwa da bin sau-da-ƙafa: Ko matakan bin sau-da-ƙafa na tsari/projen yana aiki sosai da fannonin nan 4 na kan gaba mafiya muhimmancin na NDH?

### 6.1 Allon auna fannoni 4 na kan gaba mafiya muhimmanci na NDH a cikin tsarin/projen HKLJH

| N° | Alamun da aka auna | Lamba cikin 5 (daga 1 zuwa 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Ƙarin bayani |
|---|---|---|---|
| ***Maida hankali ga gungun mutane marasa galilhu*** | | | |
| 1 | Tsarin ya ƙumshi gungun marasa galihu, waɗanda aka manta da su, | | |
| 2 | Ana lura da dalilai na ainahi, da waɗanda suka shafi al'adu da suke sa wariya, da rashin galihu mai nasaba da siyasa, ma'ikantan wuri (ko ya zamana babu su) cikin tsari/proje | | |
| 3 | Tsari/proje yana rubucewa, yana kuma adana irin ribar da marasa galihu ko waɗanda aka manta da su, suke samu | | |
| 4 | Ana lura da al'amarin jinsi cikin nazarin bukatun marasa galihu ko waɗanda aka manta da su | | |
| 5 | Ana yi a kowa adalci cikin nazarin bukatun marasa galihu | | |
| | ***Jimilla ta 1*** | | |
| ***Maida hankali ga dalilai na ainahi*** | | | |
| 6 | Tsari/proje yana bayana halin da ake ciki ta wurin tilasa ma al'umma ta yardar ma kowane mutum ko gungun mutane sau more ma hakinsu. | | |
| 7 | Tsari/proje yana lura dukan hakin mutane dangance matsalolin da aka hanga | | |
| 8 | An kafa matakan aiki tare da masu faɗa a ji game da siyasar aiki da ɗaukar ƙuduri dangance da matsalolin da aka hanga | | |
| 9 | An ba mutane damar su faɗaɗa zaɓe da iyawarsu ta more ma hakinsu da ƴancinsu | | |
| 10 | Ana warware matsalolin da aka hanga tare da lura da wurin da ake, cikin ƙasa da kuma sauran ƙasashe | | |
| | ***Jimilla 2*** | | |
| ***Aiki da masu haki, da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin*** | | | |
| 11 | Ana aiki da shawarwarin ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa na kare hakin ɗan Adam suka bada | | |
| 12 | An san ko su wanene masu hakin da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin, | | |

| N° | Alamun da aka auna | Lamba cikin 5 (daga 1 zuwa 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Ƙarin bayani |
|---|---|---|---|
| | da ƙarfafa iyawarsu ta ƙwato hakin nasu | | |
| 13 | Ana lura da bukatun masu wajibin tilasa a kiyaye hakin mutane, domin su a ba su damar cika aikinsu zuwa ga masu hakin. | | |
| 14 | Masu wajibin tilasa a kiyaye hakin mutane suna da nauyin bada lisafi kamar yadda doka da siyasar aiki suka tanada dangance da matsalolin da aka hanga | | |
| 15 | An kawas da matsloli masu nasaba da dokoki da tafiyar da aiki, daga gaban mutane domin a yardar masu su ƙwato hakinsu. | | |
| | ***Jimilla ta 3*** | | |
| ***Maida hankali ga iya yi wa kai*** | | | |
| 16 | Waɗanda ke cikin aikin (masu amfana da aiki, ma'aikatun gwamnati ƘFH, Masu zuba jari) suna cikin masu shimfiɗa dubaru da guri | | |
| 17 | Sa hannu cikin aiki, guri ne da tsarin/projen ke hange | | |
| 18 | An shimfiɗa matakan bada lisafin samakon aikin da aka aiwatar | | |
| 19 | An shimfiɗa matakan bada lisafi na masu wajibin tilasa a kiyaye hakin mutane | | |
| 20 | An bunƙasa tsarin ƙawance domin tabbatar da kuzarin da ake bukata cikin aikin. | | |
| | ***Jimilla ta 4*** | | |

### 6.2 Allon auna yanayin tsari/projen HKLJH dangance da NDH

| N° | Alamun da aka auna | Lamba cikin 5 (daga 1 zuwa 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Ƙarin bayani |
|---|---|---|---|
| ***Maida hankali ga gungun mutane marasa galihu*** | | | |
| 1 | Nazarin ya ɗauki gungun mafiya rashin galihu tamkar abu na farko | | |
| 2 | Nazarin yana bada fassara rashin galihu marasa galihu, da matsalolinsu | | |
| 3 | Nazarin yana fassara yadda ake taka hakin mutane, da irin yadda ake taka hakin marasa galihu | | |
| 4 | Nazarin yana sa a ɗauki marasa galihu a matsayin gungun farko ko na biyu a cikin tsari mai zuwa | | |
| 5 | Nazarin yana samun bayanai na yanzu | | |
| | ***Jimilla ta 1*** | | |
| ***Maida hankali ga dalilai na ainahi*** | | | |
| 6 | Nazarin yana bada ganewa ta gaba ɗaya game da matsalolin da aka gano da su | | |
| 7 | Nazarin yana gano da dalilai da matsalolin da ake gani nan take | | |
| 8 | Nazarin yana bada bayani a kana siyasar aiki, dokoki, da farilai, da tabi'u da sanin da ake da shi game da matsalolin da aka hanga | | |
| 9 | An fassara yanayin dokoki da na siyasa na matsalolin da aka hanga | | |
| 10 | An fassara dalilai na ainahi na irin yadda ake taka hakin ƴan Adam | | |
| | ***Jimilla ta 2*** | | |
| ***Aiki da masu hakin da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin*** | | | |
| 11 | Nazarin yana sansancewa da abubuwan da ake so, iyawa da iko na waɗanda | | |

| N° | Alamun da aka auna | Lamba cikin 5 (daga 1 zuwa 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Ƙarin bayani |
|---|---|---|---|
| | ke cikin aikin dangance da matsalar a matsayinsu na masu hakin | | |
| 12 | Nazarin yana sansancewa da abubuwan da ake so, iyawa, da ikon waɗanda ke cikin aikin, dangance da matsalar, a matsayinsu na masu hakin da masu wajibin a tilasa kiyaye hakin. | | |
| 13 | Nazarin yana sansacewa da masu wajibin tilasa kiyaye hakin (ta fannin doka ko sanin ya kamata) da masu hakin yadda ya kamata | | |
| 14 | Nazarin ya nunawa ko masu aikin sun sani kuma su yarda da hakinsu, da kuma wajibinsu, da kuma ko suna da ƙarfin ƙwato hakinsu, ko kuma ba sa iyawa | | |
| 15 | An sansace, kuma an auna matakan kan ƙara | | |
| | ***Jimilla ta 3*** | | |
| ***Maida hankali ga iya yi wa kai*** | | | |
| 16 | Waɗanda ke cikin aikin suna cikin shirin rubuta nazari, kuma ana neman shawara gare su game da maƙasudi da shawarwari | | |
| 17 | Matakan sa hannun waɗanda ke cikin aiki da abukan aiki, ya ƙarfafa da taimakon ƙungiyoyi masu ƙarfafawa, da matakan mayar da bayanai | | |
| 18 | Nazarin yana sansance hanyoyin da za su ƙarfafa sa hannun talakawa cikin aikin, da iya sarrafa kayan aikin da suke da su | | |
| 19 | Nazarin yana sansance da gungun da ƙawancen aiki, da kuma dubarun na kuzarantar da talakawa | | |
| 20 | An fayyace bukatu na iya yi wa kai na masu hakin da kuma masu wajibin tilasa a kiyaye hakin | | |
| | ***Jimilla ta 4*** | | |

### 6.3 Allon auna ingancin tsari/projen HKLJH dangance da NDH

| N° | Alamun da aka auna | Lamba cikin 5 (daga 1 zuwa 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Ƙarin bayani |
|---|---|---|---|
| ***Maida hankali ga gungun marasa galihu*** | | | |
| 1 | Gurin tsarin/projen yana ɗauke da abubuwan kan gaba mafiya muhimmanci da marasa galihu suka sanas su da kansu | | |
| 2 | Tsari/projen yana kyautata a yi aiki tare da marasa galihu | | |
| 3 | Sakamakon tsari/projen yana sa a inganta halin hakin ɗan Adam domin marasa galihu | | |
| 4 | Tsari/projen yana sa rarrabe bayanai dangance da marasa galihu game da matsalolin da aka hanga | | |
| 5 | Tsari/projen yana kyautata iya yi wa kai na marasa galihu | | |
| | ***Jimilla ta 1*** | | |
| ***Maida hankali ga dalilai na ainahi*** | | | |
| 6 | Tsarin yana kula da dalilai na ainahi, da sakewa yanayin siyasar aiki, dokoki waɗanda aka zaɓa a matsayin abubuwan kan gaba mafiya muhimmanci. | | |
| 7 | Gurin tsari sun da nasaba da dokoki da farilan hakin ɗan Adam | | |
| 8 | Ana lura da wuri, da ƙasa, da ƙasashe cikin aikin da ake aiwatar da shi | | |
| 9 | Hanyoyin sadarwa na aikin da ake aiwatar da shi, suna ƙumsar waye ma mutane kai a kan dalilai na ainahi dangance da matsalolin da aka hanga | | |
| 10 | Abin da tsari/projen ya ƙumsa ba ya kyautata nuna ƙyama da wariya cikin zamantakewa da ala'du | | |
| | ***Jimilla ta 2*** | | |
| ***Aiki da masu hakin, da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin*** | | | |
| 11 | Tsarin yana nuna sakewa wajen masu hakin, dangance da iya yi wa kai da | | |

| N° | Alamun da aka auna | Lamba cikin 5 (daga 1 zuwa 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Ƙarin bayani |
|---|---|---|---|
| | shiga cikin mutane | | |
| 12 | Tsarin yana nuna sakewa wajen masu wajibin tilasa a kiyaye hakin, dangance da ƙarfafa wajibin nasu, da yunƙurinsu | | |
| 13 | Ayukan tsari/projen sun kafu bisa hulɗa tsakanin masu haki da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin. | | |
| 14 | Ayukan tsari/projen suna ƙarfafa aiki tsakanin masu hakin da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin, cikin sassan aiki, suna haɗa ƙanan abubuwa da manya | | |
| 15 | Ayukan tsari/projen suna kafa sassa da iyawa domin masu haki da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin | | |
| | ***Jimilla ta 3*** | | |
| ***Maida hankali ga iya yi wa kai*** | | | |
| 16 | Tsarin yana aiki da ka'idodi da guri sanannu, kuma masu haske | | |
| 17 | Shirin tsarin yana ɗauke da matakai na masamman domin tabbatar da kula gungun mutane marasa galihu, da sa hannun masu aikin yadda ya kamata | | |
| 18 | Tsarin yana aza matakan kan ƙara da gyara al'amura, waɗanda ana iya amfani da su cikin gida ko waje domin haɗa masu wajibin tilasa a kiyaye hakin mutane da ma'aikatun da abin ya shafa | | |
| 19 | Tsarin yana ƙarfafa bunƙasa ƙirkiro da ƙawance domin masu haki su iya ƙwato hankinsu | | |
| 20 | Tsarin yana neman ya ƙarfafa yin aikin da kowa, da wajibin masu hakin ta wurin waye ma mutane kai, da ƙarfafa iyawarsu, da cigaba na gaba ɗaya, da kuma ƙarfafa neman afuwa | | |
| | ***Jimilla ta 4*** | | |

### 6.4 Allon auna ingancin matakan bin sau-da-ƙafa na tsari/projen HKLJH dangance da NDH

| N° | Alamun da aka auna | Lamba bisa 5 (daga 1 zuw 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Commentaires |
|---|---|---|---|
| ***Maida hankali ga gungun marasa galihu*** | | | |
| 1 | Ana ɗaukar gungun mutane da aka hanga tamkar masu haki, amma ba masu amfana kaɗai ba | | |
| 2 | Ana ba marasa galihu damar su tsara kansu, kuma su kuzarantar da kansu da kansu | | |
| 3 | Hanyar aiwatar da aiki ba ta kyautata nuna ƙyama da wariya cikkin zamantakewa da al'adu | | |
| 4 | Ana sa marasa galihu cikin matakan bin sau-da-ƙafa | | |
| 5 | Ana lura da bukatu da damuwar da marasa galihu suke da su ciki matakan bin sau-da-ƙafa | | |
| | ***Jimilla ta 1*** | | |
| ***Maida hankali ga dalilai na ainahi*** | | | |
| 6 | Ana kafa hulɗar aiki da ƙawance tare da kafofin yaɗa labarai da sauran ƙungiyoyin fara hula domin a kai matsayi mafi inganci | | |
| 7 | Sakamakon bin sau-da-ƙafa suna sa a ƙara neman sakewa | | |
| 8 | Bin sau-da-ƙafa yana lura da siyasar aiki ta wuri, da ta ƙasa, da ta ƙasashe | | |
| 9 | Ana rubuce sakewar da masu wajibin kiyaye hakin mutane suka samu | | |
| 10 | Bin sau-da-ƙafa yana rubuce sakewar da aka samu game da duban da marasa galihu suke da zuwa ga dalilai na ainahi | | |
| | ***Jimilla ta 2*** | | |
| ***Aiki da masu hakin da kuma masu wajibin tilasa kiyaye hakin*** | | | |
| 11 | Akwai taɗi mai muwafaka tsakanin masu wajibin tilasa a kiyaye | | |

| N° | Alamun da aka auna | Lamba bisa 5 (daga 1 zuw 5, inda 5 ce lamba mafi girma) | Commentaires |
|---|---|---|---|
| | hakin | | |
| 12 | An kafa matakan tsaro da lura domin kada a sami rikici cikin hulɗa | | |
| 13 | An kafa ƙaƙƙarfan matakan da suke haɗa masu hakin da masu wajibin tilasa a kiyaye hakin | | |
| 14 | An rubuce yadda ake kula da bukatun masu wajibin tilasa a kiyaye hakin mutane ta fannin doka, cikin aikin bin sau-da-ƙafa | | |
| 15 | An rubuce yadda ake kula da bukatun masu wajibin tilasa a kiyaye hakin mutane ta fannin sanin ya kamata, cikin aikin bin sau-da-ƙafa | | |
| | ***Jimilla ta 3*** | | |
| ***Maida hankali ga iya yi wa kai*** | | | |
| 16 | Masu hakin da waɗan da ke cikin aikin suna cikin aiwatar da aikin, da bin sau da ƙafa na tsari/proje | | |
| 17 | An kafa matakan bada bayanai domin a yardar ma masu hakin su sa hannu cikin aikin tare da sanin abin da ake ciki | | |
| 18 | Ana aiki da ka'idodin hakin ɗan Adam cikin matakan aiwatar da tsari/proje | | |
| 19 | An tabbatar da wajbi da yin aiki cikin haske ta wurin aiki da ka'idodin ƙungiya, da na aiwatar da aiki, da tsarin isar da bayanai ma ƙwari | | |
| 20 | Masu hakin suna ƙara yin la'akari da hakinsu, sun fi iya tsara kansu, sun fi iya neman ƙwato hakinsu yadda ya kamata | | |
| | ***Jimilla ta 4*** | | |

## 7. Wa ke iya amfani da wannan alluna, kuma yaya ake amfani da su ?

Ƙungiyoyi da mutanen da suke aiki cikin tafiyar da tsari/projen HKLJH, suna iya aiki da waɗannan alluna, ko cikin ma'aikatun fusahar aiki na gwamnati, ko abukan aiki masu zuba jari, ko cikin ƙungiyoyin fara hula (Ƙungiyoyi Masu zaman Kansu, wasu ƙungiyoyi, gungun mutane da suka tsara kansu, da)

Shugaban tsarin HKLJH yana iya auna tsari da proje ta wurin amfani da waɗannan alluna guda guda. Wani abokin aiki da yake aiki cikin HKLJH na iya amfani da su lokacin zaman taro na ƙara wa juna ilimi. Daga ƙarshe, wani mashahuri na iya amfani da su idan akwai hali.

## 8. Maƙasudi

Wannan kundi koyaswa na gabatar da NDDH, tamkar wata hanya da ta dace, kuma mai ɗorewa ta warware matsalolin da ake fuskanta game da aikin HKLJH, masamman domin marasa galihu, ko waɗanda aka ware/manta da su, dangance samun kulawa ta fannin kioyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa.

Kundin koyaswa ya ƙumshi kayan aiki masu inganci da za su taimaka ma masu tafiyar da tsari/projen HKLJH dangance ga NDDH cikin aikin bunƙasa HKLJH domin marasa galihu.

Muna begen cewa idan masu aiki cikin HKLJH, suka yi amfani da NDDH, za a sami biyan bukata mai ɗorewa dangance da kiyon lafiya da ya shafi jima'i da haifuwa.

**Abubuwan da ake iya dubawa**

Boesen, Kirkermann Jakob and Martin Thomas. *Applying a Rights-Based Approach: An inspirational Guide for Civil Society*. Kopenhagen: The Danish Institute for Human Rights, 2007.

http://www.operationspaix.net/67-lexique-groupes-vulnerables.html (consulté le 15 Août 2019)

https://www.larousse.fr/dictionnaires/francais/exclu_exclue/32016 (consulté le 16 Août 2019)

https://www.ohchr.org/FR/Issues/Pages/WhatareHumanRights.aspx (consulté le 19 Août 2019)

## Expressions dans page de garde

| | |
|---|---|
| Analyse causale basee sur les droits : | Nazarin dalilai dangace da haki |
| Droits non respectes/realises: | Hakin da ba a kiyaye ba |
| Causes immediates: | Dalilai na take-yanke |
| “Statut de la personne versus ses droits: | “Matsayin mutum a gaban hakinsa” |
| Causes sous-jacentes | Dalilai na ɓoye |
| “Service, acces, pratiques: | “Kulawa, samun kai ga kulawa, abin da ke faruwa” |
| Causes fondamentales/structurelles: | Manyan dalilai |
| “Societes, politiques, ressources: | “Al’umma, siyasar aiki, kayan aiki” |